# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Elisha, Mutum Mai Al’ajibai

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**



**Babu isashen shanun da za su ja garma. Ana bukata guda daya.**



**Wannan bai tsai da wani saurayi manomi mai suna Elisha ba! Shi dai ya hadda kai da shanun, sai ya dauki matsayin guda dayan da ake bukata. Dole babu shakka shi mai karfi ne, mai wayo mai kwazon aiki.**



Sa'ad da Elisha yana noma, annabin Allah Iliya ya zo ya kira shi. Dan saurayin ya bar gonarsa don ya zama dan hidimar Allah. Wata rana Allah ya dauki Iliya zuwa sama a cikin gugguwa. Yanzu Elisha ya zama annabin Allah ga Isra'ila.

3



Ko da yake Elisha yana bakin ciki cewa Iliya ya tafi, ya yi addu'a Allah ya ba shi iko kamar na Iliya. Elisha ya dauki alkyabbar Iliya, sai ya buga ruwa kogi mai gangarowa kamar yadda Iliya ya yi.

Ruwan ya rabu kashi biyu! Yanzu Elisha ya sani Allah yana tare da shi.

4



Yayinda Elisha yana tafiya zuwa wani gari mai suna Betel, wadansu matasa suka yi masa gori, suna kira, "Haura sama, kai mai kan angulu!" Ba su damu ko Elisha bawan Allah ba ne. Sai wani abu mai ban tsoro ya faru da su. Sai namomin daji biyu suka bullo suka cinye matasan nan guda arbain da biyu.

5

Wata rana Elisha ya sadu da wata gwauruwa wadda ake bin ta bashi kuma ba ta iya biya ba.



Don ya samu kudinsa, wanda yake bin ta kudin zai dauki 'ya'yanta biyu don su zama bayinsa. "Tafi, yi arrow jerikoki daga makwabtanki ... wadand babu kome a ciki," Elisha ya gaya mata. Allah zai yi abin mamaki wa gwauruwar nan.

6

Gwauruwar tana da jerikan daya ne na mai a gidan. Amma daga wannan karamin jerikan ta zuba wa sauran jerikokn mai cike. Da a ce suna da manyan kwanon da ake wanka a zamaninmu, a ganinka da Allah ya ciccika su? Gwauruwar ta sayar da mai din sai ta cece yaranta.



7

Wata kuma da maigidanta sun gyara wani daki na musamman a gidansu don Elisha ya shiga ya huta duk lokacin da yake wucewa a wurin. A dakin sai suka sa gado, da teburi, da kujera, da abin ajiye fitila. Dakin nan na Elisha ne na musamman.



8

Elisha yana ta tunani yadda zai biya wannan iyali saboda kirkinsu. Da ya ji cewa ba su da 'ya'ya, sai ya fada wani abu wanda matan ba ta yarda da shi da sauri ba. "Lokaqci kamar haka a shekara mai zuwa, za ku rungume yaronku."
Tabas, bayan shekara daya, an haifi jaririn.



9

Bayan an samu dan shekaru, yaron yana tare da babansa a filin gona. "Kai na, kai na," yaron na kuka. Da aka kawo yaron wa mamansa, ya zauna a gwiwanta har zuwa tsakar rana, sai ya mutu. Maman ta ajiye gawan yaron a dakin Elisha. Wane ne a ganinka zai taimake ta?



10

Ka ce Elisha? Haka yake! Ta shirya jaki ta ruga nemansa. Elisha ya zo gidanta, ya haura dakin samashe kadai ya yi addu'a ga UBANGIJI. Allah yadawo da rai na yaron. Elisha ya kira matan ya ce, "Dauki yaronki."
Ina misalin rin farin cikinta!



11



A wani kasa kusa da Siriya akwai wani Babban soja mai suna Naaman. Yana da karfi hali da karfi, amma yana da mummunan ciwon fatan jiki mai suna kuturta.

12

Matan Naaman tana da wata yarinya mai yi mata hidima wadda aka kama daga Isra'ila. Wannan yarinyar ta ce, "Da Naaman yana tare da annabin da yake a Isra'ila mana! Da zai warkar da shi kuturtarsa."



13

Nan da nan Naaman ya kama hanya do ganin annabin. Ya dauki azurfa, zinariya, da riguna masu kyau don mika kyauta.



14



Dan hidimar Elish ya fita waje ya ce, “Je ka yi wanka a Kogin Yodan sau bakwai za ka warke.” Naaman ya yi fushi. Ba zai iya wanka a ruwaye mau tsabta na garinsa a Siriya ba. Cikin fushi ya komaya kama hanya zuwa gidansa.





Abin da ya taimake Naaman shi ne, ‘yar hidimarsa suka yi masa magana sai ya yi biyayya da abin da Elisha ya gaya masa. Sai Naamman ya tafi ya soma jikijnsa a cikin Kogin Yodan sau bakwai. Sai Naaman kuturu ya warke! Sa’an na Naa, an ya yi sujada ga Allah na gaske, Allah na Elisah, UBANGIJI wanda ya warkar da shi daga kuturta.





Allah ya y amfani da bawansa Elisha hr ma bayan da ya mutu. Wata rana, an binne wani mutum a kogon da aka binne Elisha tuntuni. Sa’ad da jikin mutumin ya taba kasusuwan annabin sai mutumin ya farka daga mutuwa ya tashi tsaye da kafafunsa. Da gaske, Allah ya nuna ikonsa ta wurin bawansa mai aminci, Elisha.



Elisha, Mutum Mai Al’ajibai

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

2 Sarakuna 2-13

“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130






25 60



Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah: Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16